# LABARAN KARYA DA CDD

## TA GANO A KARSHEN SATIN 21 GA WATAN FEBRAIRU SHEKARA NA 2021

Labarin bogi ko labarin karya labari ne da ba'a tantance shi ba. Yakan iya zama labari da aka buga wanda ba abi ka'idar da ya kamata a bi ba wajen wallafa labarin kuma a ka yada shi a kafafen yada labarai.

A wannan satin CDD ta gano wasu labarai dake yawo a kafafen yada labari wanda suka hada da tallafin daga gidauniyar Dangote da kuma wani shafi a manhajar twitter da ke alakanta kansa da ma'aikatar matasa da wasanni ta tarayya.

A ranar Talata, 16 ga watan Fabrairun shekara ta 2021, masu tantance sahihancin labarai na Cibiyar Bunkasa Demokaradiyya da Cigaba (CDD) sun gano wani sakon da ake yadawa ta manhajar WhatsApp da ke ikirarin cewa Gidauniya Aliko Dangote na bada tallafi dan fara sana'o'i ga 'yan Najeriya da suka cancanta.

Sakon yace: "Ku gaggauta dubawa dan sanin ko kun cancanta da samun tallafin kudi daga tsarin bada tallafi na Gidauniyar Dangote na shekara ta 2021"

Binciken da CDD ta gudanar game da ikirarin tallafi daga Gidauniyar Dangoten ya gano cewa sakon da ake yadawa din sakon karya ne.

Adireshin yanar gizon da aka bayar dan yi rijista, adireshi ne na bogi. Haka zalika, hoton da aka lika a jikin sakon babu shi a adireshin yanar gizon da aka bayar dan yin rijistar, hakan wani sabon salo ne na jan hankali da yaudaran mutane tare da zambatar su. Kuna iya karanta cikakiyar bayani a *nan*




A ranar 17 ga watan Fabrairun shekara ta 2021, ayarin wasu yan kishin kasa sun janyo hankalin masu tantance sahihancin labarai da bankado labaran bogi na Cibiyar Bunkasa Demokaradiyya da Cigaba (CDD) game da wani shafin Twitter mai lakabin "Nigerian Youth Investment Fund" (*NYIF_NGR*) da ke ikirarin cewa shi wani tsari ne na bada tallafi ga sana'o'in matasa da gwamnatin tarayyara Najeriya ke goyon baya.

Masu lura da shafin sunyi kira ga wadan da ke bukatar tallafin fara sana'a su biya wasu kudade kafin samun tallafin.




Binciken da CDD ta aiwatar ya gano cewa ma'aikatar matasa da bunkasa harkokin wasannin ba ta umarci masu neman kowane irin tallafi su biya kudi ba, dan haka da'awar @NYIF_NGR cewa a biya kudi karya ne.

Tsarin tallafawa matasa da jari da ma'aikatar matasa da bunkasa wasanni ta fito dashi ya kammala shirin somin-tabi a watan Yuli na shekarar da ta gabata inda mutane 239 suka amfana da N165,700,000.

Shafin gaskiya na Twitter da ke bada bayanai game da harkokin matasa na gwamnatin tarayya shine @NYIF_NG. Domin karanta cikkayar labarin *latsa nan*

## Wasu daga ciki labaran bogi da CDD suka wallafa

*Shin Gwamnatin Tarayya Ta Amince Da Yin Rijistar NIN Ta Hanyar Yanar Gizo?*

*Bill Gates Bai Ce Za'a "Sake Samun Wata Annoba Bayan Cutar Korona Ba*"

*Gwamnatin Jahar Kano Ba Ta Rushe Makarantar Sheikh Abduljabbar Ba!*

*Shin WHO Dakatar Da Najeriya Daga Neman Maganin Rigakafin Cutar Korona?*

CDD is urging Nigerians to always verify the authenticity of stories before sharing them.

You can forward suspicious messages for verification via +2349062910568 or contact us on twitter @CDDWestAfrica

#StopFakeNews #StopDisinformation

Center for Democracy and Development West Africa| CDD West Africa

Centre for Democracy & Development
Centre pour la démocratie et le développement

The Centre for Democracy and Development (CDD) was established in the United Kingdom in 1997 as an independent, not-for-profit, research training, advocacy and capacity building organisation

**Address**
16 A7 Street, Mount Pleasant Estate, (CITEC) Mbora District- Jabi Airport Road,Abuja

**Phone No**
+23492902304

**Email**
cdd.abv@cddwestafrica.org

**Website**
www.cddwestafrica.org